JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 4 Jimada al- Ah-khir, 1443

MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI ٧ Junairu, 2022

(١)

## AIKIN YI DARAJA NE

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: ku yi aiki kawai, da sannu Allah da Manzonsa da sauran muminai za su gani, da kuma sannu za a komar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye, da waɗanda suke a fili, shi kuma zai ba ku labarin dukan abubuwan da kuke aikatawa)** [at- Tauba: 105], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci yana yi wa aiki kallo mai muhimmanci, da girmamawa na musamman, aiki shi ne hanyar cigaba da samun ɗaukaka, duk wanda yake yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na tsanaki, zai ga irin yanda yake kira ƙarara zuwa ga yin aiki wanda da shi ne ake sami daman raya doron ƙasa, da kuma samar wa duniya da dukan alhairi, Allah mai girma yana cewa: **(Shi Allah ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta..)** [Hudu: 61], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Shi ne wanda ya sanya ƙasa ta zamo maku sauƙaƙƙa, ku yi tafiya a sasanninta, ku ci daga cikin arzikin Allah da ya fitar maku daga gareta, zuwa gare shi -shi kaɗai- za ku koma domin sakamako**) [al- Mulki: 15], Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na**

**alhairi a duniya da lahira)** [al- Juma'a: 10], Saboda muhimmancin da aiki yake da shi ne Allah ya bayar da umurnin a yi shi bayan ya bayar da umurnin a yi Sallah kai tsaye, a duk sanda Sayyiduna Arak Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) ya yi sallar juma'a, ya miƙe zai fita, yakan tsaya a ƙofar Masallaci, ya ce: **"Ya Ubangiji Allah, na amsa kiran ka, na yi sallar farilla da ka farlanta, na kuma tashi zan shi biɗa kaman yanda ka bayar da umurni, ina roƙon ka azurta ni da falalarka, kai ne fiyayyen mai azurtawa".**

Haka ma Hadisan Annabi cike suke da kira zuwa ga gabatar da aiki, da kuma yin himma tuƙuru a cikin sa, ganin cewa aiki girma ne da daraja da yake kiyaye karamar ɗan Adam, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Fiyayyen nema shi ne kasuwanci na gaskiya da gaskiya, da kuma aikin da mutum ya yi da kansa),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mutum ya tafi ya yi icce ya ɗaura a bayansa ya fi alhairi akan ya rinƙa roƙon mutane, su ba shi ko su hana shi)**, Sufyannus Sauriy (Allah ya ƙara masa rahama) yakan bi wurin wasu mutane da suke a Masallaci mai alfarma suna zaune, sai ya tambaye su: **Mene kuke yi? Sai suka ce masa: mene kuwa za mu yi?!, Sai ya ce: Ku je ku nemi arzikin Allah, kada ku zama nauyi akan wuyan Musulmai.** Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **Kada wani daga cikin ku ya zauna ba tare da sana'a ba, ya rinƙa cewa: Ya Ubangiji Allah, ka azurta ni, lallai kun riga kun sani cewa sama ba ta ruwan zinariya ko azurfa..**

Saboda daraja, da kuma muhimmancin da aiki yake da shi ne su kansu Annabawa masu tsira da aminci suka kasance masu sana'a, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Annabi Dawud –AlaiHiS Salam- yana cin guminsa ne),**

yana kuma cewa: **(Annabi Zakariyya -AlaiHis Salam- kafinta ne)**, shi ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana yin aiki da kansa, ya kuma hidimta wa iyalansa, Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da kansa yake gyara takalmin sa, ya kuma ɗinke tufafinsa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi kira da mu kama sana'a mu kuma gabatar da aiki koda kuwa a mintin ƙarshe ne na rayuwar mu, mai tsira da aminci yana cewa: **(Idan za a tashi alƙiyama ya zama a lokacin akwai iccen dabino a hannun wani daga cikin ku, idan dai har ya sami daman ya dasa shi kafin a tashi alƙiyama, to ya yi).**

Saboda da darajar da Shari'ar Musulunci ta bai wa aiki ne ta sanya wanda yake faɗi tashin neman arzikin da zai inganta rayuwar sa da na 'ya'yan sa ya zama daidai yake da shahidi, lallai Alƙur'ani mai girma ya gwama tsakanin aiki da sadaukar da rayuwa saboda ɗaukaka kalmar Allah, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Wasu kuma suna ta kai-komo wajen kasuwanci da aiki suna neman arzikin Allah..)** [al- Muzammil: 20], Haka ma lokacin da wani mutum ya wuce ta gaban Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), Sahabban sa suka ga juriyar sa da ƙoƙarin sa, sai ya burge su, sai suka ce: Ina ma wannan abu da yake yi, yana yi ne saboda Allah?! Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Idan yana kai komonsa ne saboda ya nema wa 'ya'yan sa ƙanana, to yana kan fisabililLahi, haka ma Idan ya fita ne saboda nema wa iyayensa biyu da suka manyanta, to shi ma yana kan fisabililLahi, idan ya fita ne saboda ya nema wa kansa saboda ya kame, to shi ma**

**yana kan fisabililLahi, Idan ya fita ne saboda iyalansa, to shi ma yana kan fisabililLahi).**

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai addinin Musulunci bai nemi kawai da mu gabatar da aiki ba, hasali ma ya kwaɗaitar da mu akan kyautata aiki saboda neman yardar Allah Mai girma da buwaya, lallai Allah Mai girma da buwaya ya yi alƙawarin lada mai girma ga wanda yake kyautata aikinsa, Allah mai girma yana cewa: **(Lallai waɗanda suka yi imani suka kuma aikata ayyuka na gari, lallai mu ba ma tozartar da ladan wanda ya kyautata aiki)** [al- Kahfi: 30], haka ma kyautata aiki yana cikin al'amurran da Allah mai girma da ɗaukaka yake so, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan wani daga cikin ku zai yi aiki da ya kyautata shi).**

Amanar aiki alhaki ne da ya rataya a wuyan kowane ma'aikaci da jami'in gwamnati, dole ne ya kula da Ubangijin sa mai girma da buwaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai Allah mai sanya ido ne akan ku)** [an- Nisa'i: 1], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), lallai ka isar da saƙo, Allah ya san haka, ba ka taɓa kasancewa a cikin wani al'amari cikin al'amurranka, haka ma ba ka taɓa karanta Alƙur'ani, ka yi aiki da shi, kai ko al'ummarka ba face mun yi maku shaida muna ganin lokacin da kuke shiga cikin domin yin jahadi, babu wani abu daidai da ƙwayar zarra a ƙasa, ko a sama da yake iya ɓuya wa Ubangijinka, kai babu abin da yake ƙasa da haka,**

**ko yake sama da haka da yake iya ƃuya. Lallai duka waɗannan abubuwan suna nan a rubuce a wurin Allah dalla- dalla**) [Yunus: 61], Lokacin da aka tambayi Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) game da al- Ihsan, cewa ya yi: **(Ka bauta wa Allah kaman kana ganinsa, domin ida kai ba ka ganinsa, to shi yana ganinka).**

**Ya Allah Ubangiji muna roƙon ka ba mu daman aikata ayyukan alhairi, ka kiyaye mana ƙasar mu da sauran ƙasashe daga dukan abubuwan ƙi..**